ARDP

Arewa Research & Development Project



# RAHOTON 2019

## KAN AYYUKAN RAYA-KASA A MAZAƁUN TARAYYA DA KE JIHAR ZAMFARA

*Da Tallafi daga:* MacArthur Foundation

# GABATARWA

Bin diddiƙin ayyukan raya-ƙasa a mazaɓun da ke Jihar Zamfara na daga cikin ayyukan Cibiyar Bincike da Ciyar da Arewa Gaba, wato "Arewa Research and Development Project" (ARDP) wadda Gidauniyar MacArthur ke tallafa wa a ƙarƙashin tsarin shirin tallafi na "On Nigeria 2.0". Ginshiƙin shirin na mayar da hankali ne kan ƙoƙarin hana ƙaruwar cin-hanci da rashawa ta fuskar taimakama shirye-shiryen ƙungiyoyin al'umma na tabbatar da aƙidojin tsare gaskiya da sa hannun al'umma cikin tsarin gudanar da mulki. Babban gurin wannan tsarin aiki shine ya auna ƙarfin sa hannun mutane wajen tantancewa da gudanar da ayyukan raya mazaɓu da kuma yin la'akari da sahihan bukatun al'ummar mazaɓun. Ana kautata zaton cewa wannan tsarin aikin zai kafa matakai ko kuma ya ƙara haɓaka hanyoyin da 'yan ƙasa zasu shiga cikin tsare-tsaren zaɓen ayyukan da kuma sa ido wajen aiwatar da su. Wannan tsarin aikin dai Kungiyar ARDP tare da haɗin guiwar Kungiyar ZamTracka ke jagorantarsa.

Kungiyar ARDP dai wata cibiya ce mai bincike da bata da alaƙa da gwamnati ko la'akari da wata siyasa, ƙabila, ko nuna bambancin addini wadda ayyukanta sun mayar da hankali wajen nazari da tantance manyan matsaloli da ke addabar Arewacin Nijeriya da al'ummarta, da yunƙurin samar da hanyoyin bincike da tsare-tsaren ayyukan da zasu magance matsalolin dake addabar yankin. Gurin Cibiyar shine ƙoƙarin samar da tafarkin bunƙasar tattalin arziki da kyautata rayuwar al'ummar yankin ta hanyoyin da zasu samar da haɗin guiwa tsakanin jama'a da hukomomin gwamnati wajen hada ƙarfi-da-ƙarfe domin ciyar da al'umma gaba.

Ita kuwa ZamTracka, ƙungiya ce mai zaman kan ta da ke Gusau a jihar Zamfar, wadda ta ke yekuwar ganin ana yin taka tsan-tsan da dukiyar jama'a a cikin mulkin jihar. Fitattun ayyukan ta sune samowa da tantance bayanai kan tanade-tanaden ayyuka da ke cikin kasafin kuɗi na jihar Zamfara da kuma ayyukan raya-ƙasa a yankunan mazaɓu, da kuma yin amfani da su wajen wayar da kan al'umma. Manufa dai ita ce a taimaka wa jama'a wajen bin diddiƙin tanade-tanade kasafin kuɗi da yadda ake gudanar da ayyukan raya-ƙasa a mazaɓu. Ana sa ran cewa wannan yunƙuri zai sa a samu masu himma da dagewa wajen ganin ana gudanar da ayyukan raya-ƙasa na gwamnati da hukumominta tare da haɓaka yadda jama'a za su nemi samun ɗorarriyar hanyar tsoma bakinsu a cikin gudanar da al'amuran jiharsu.

# KARIN HASKE

Ayyukan raya-ƙasa na mazaɓu wasu ayyuka ne da wakilai a majalisun dokoki na tarayya ke ƙirƙirowa domin kawo ribar mulkin demokaraɗiyya ga al'ummominsu don haɓakar ci-gaban yankunan karkara. A kan gabatar da bukatun gudanar da waɗannan ayyukan ne ga sashen mulki a lokacin da ake tsare-tsaren kasafin kuɗi. Tsarin mulkin ƙasa ya tanadi cewa majalisun tarayya ke da alhakin sanya ido akan ayyukan gwamnati. Kasancewar 'yan majalisu ne ke ƙirƙirar ayyukan, ashe su ke da nauyin su riƙa yiwa jama'a bayanai akai-akai akan ayyukan. Wannan ya isa hujja saboda talakawa ba za su iya tunkarar hukumomin gwamnati cikin sauƙi ba kamar yadda za su iya tuntuɓar wakilan su. Domin ganin munbi diddiƙin waɗannan ayyukan raya ƙasa akan kari, mun yi amfani da jami'an mu waɗanda suka san wuraren da ake gudanar da takamaiman ayyukan.

A sakamakon hukuncin Kotun Koli wanda yayi sanadiyyar samun sababbin 'yan majalisun tarayya daga Jihar Zamfara, ya kasance waɗannan 'yan majalisar ba su ne suka gabatar da ayyukan wannan shekarar da ake batu a kai ba. An riga an amince da kasafin kuɗin Gwamnatin tarayya tun kafin waɗannan 'yan majalisa su kama aiki, saboda haka, ba za'a a tuhume su akan tantancin ayyukan a mazaɓu ba. Amma duk da haka, doka ta tanadi cewa sune ke da alhakin tabbatar da an gudanar da ayyukan da gamsuwa.

A shekarar 2019 an ware jimillar kuɗi Naira miliyan dubu ɗaya da miliyan ɗari huɗu da ashirin (N1.42 bn) domin gudanar da ayyuka a mazaɓun tarayya na Jihar Zamfara. Si dai kuma ma fi yawan ayyuka na bayar da tallafi ne da wayar da kan jama'a amma ba manyan ayyukan raya-ƙasa ba. Hakan na tabbatar da cewa ba'ayi la'akari da bukantun al'ummar mazaɓu ba, shi yasa mafi yawan ayyukan basu da alaƙa da manyan bukatun mazaɓun. Wani abin damuwa shine zaton da al'ummomin yankunan mazaɓu ke yi na ɗaukar ire-iren waɗannan ayyukan akan garaɓasa ce daga aljifan 'yan majalisunsu wanda ke hana su neman haƙƙinsu na sanin abinda ke gudana da tabbatar da tsare gaskiya wajen zaɓen ayyukan da aiwatar da su

A ƙarshe, halin rashin tabbacin tsaro a Jihar na yin tarnaƙi wajen tantance waɗansu ayyukan musamman a yankunan da ke ƙarƙashin yankin mazaɓar ɗan majalisar dattawa ta arewa wanda da suka haɗa da Kananan Hukumomin Zurmi da Shinkafi da Birnin Magaji.

# DALLA-DALLAR KIDIDDIGAR AYYUKA

| 16 | 5 | 2 | 2 |
|---|---|---|---|
| Waɗanda Aka Aiwatar | Waɗanda bamu bi ba | Waɗanda Ba A Gano Ba | Waɗanda ba ayi ba |

# 25

## JIMILLAR AYYUKA

# MAZAƁAR ƊAN MAJALISAR DATTAWA TA ZAMFARA TA TSAKIYA

SUNAN AIKI: **Kammalawa da Sanya Kayayyaki a Asibitin 'Yandoton Daji da ke Karamar Hukumar Tsafe a Jihar Zamfara**

KUƊIN AIKI: **N224.28M**

MATSAYIN AIKI: **An kammala amma ba a sanya kayayyaki ba**

A bara ne aka fara wannan aiki wanda tsohon ɗan majalisar dattawa na yankin, Sanata Kabiru Marafa ya gabatar. A lokacin bin sawun aikin har an aiwatar da kusan rabin shi.

Muna kewar wannan aikin ganin cewa ƙaramar hukumar bata samu kula ba daga gwamnatin tarayya kuma babbar asibitin jihar na matuƙar neman taimakon kayan aiki. Mutanen wannan ƙaramar hukuma sukan daddaƙi hanya ne zuwa babban birnin jiha, Gusau, domin neman kula da lafiyarsu. A bisa wannan dalili, amfanin wannan aiki ba sai an nanata ba. Wannan aiki zai rage cinkoson mutane a cibiyoyin kula da lafiya na cikin hedkwatar jihar.

Ma'aikanmu sun fara ziyarar wannan aiki a cikin watan Janairun 2020 kuma suka bada rahoton cewa aikin na gudana sosai. A wata ziyarar da ta biyo baya har an kammala gini da sa kayan ado da fenti. Tun a watan Janairun 2021 an kammala wannan asibiti, sai dai abin takaici, har yanzu ba'a sanya kayan aiki ba, a halin yanzu asibitin na garƙame ne da kwaɗo.







# MAZAƁAR ƊAN MAJALISAR DATTAWA TA ZAMFARA TA YAMMA

SUNAN AIKI: **Sanya Fitilun Lantarki mai aiki da Hasken Rana da Injunan Taransifoma Biyu a Yankin ƙaramar Hukumar Bakura ta Jihar Zamfara**

KUƊIN AIKI: N214.28M

MATSAYIN AIKI: **Ba a san inda aka gudananar da aikin ba**

Yankin Karamar Hukumar Bakura na daga cikin yankunan da suka fi zama koma-baya a Jihar Zamfara, kuma mai ƙarancin ayyuka raya-ƙasa na Gwamnatin Tarayya a yankin. A mafi yawancin yanki babu wutar lantarki, da hanyoyi, da wuraren kiyon lafiya. Ma'aikatanmu ba su iya tantance inda wannan aiki ya ke ba - kuma wannan shine gagurumar matsalar da ƙungiyoyin al'umma ke ƙorafi akai wajen bin diddiƙin ayyukan mazaɓu.

Bayan tattunawa da muka yi da al'ummomi daban-daban na yankin, mun fahimci cewa wannan yankin bai samu kyakkywan wakilci a Majalisar Tarayya ba. Babu wani aikin raya-ƙasa guda ɗaya da mutanen yankin zasu iya nunawa a cikin shekaru goma da suka wuce. A kasancewar haka Ma'aikatan mu sun rarraba takardu da ke ƙunshe da bayanan ayyukan raya-ƙasa na mazaɓu na shekarar 2019 ga al'ummar yankin domin faɗakarwa.

# MAZAƁAR TARAYYA TA KAURA/BIRNIN MAGAJI

SUNAN AIKI: **Shirin Wayar Da-Kai ga Matasa da Mata a Mazaɓar Tarayya ta Kaura/Birnin Magaji**

KUƊIN AIKI: N35M

MATSAYIN AIKI: **Ba a yi ba**

Ma'aikatun mu basu iya tantance aiwatar da wannan aiki ba. Ma'aikatan sun tuntuɓi al'ummar wannan mazaɓa amma basu sami wani bayani da ya yi kama da shirin aiwatar da aikin ba duk da cewa aikin na cikin tsarin ayyukan da aka gabatar a shekarar 2019. Duk da haka, Kungiyar ZamTracka zata ci gaba da bin sawun wannan aiki tare da ɗaukar matakan da suka dace wajen ganin anyi ma wannan mazaɓa adalci.

# MAZAƁAR ƊAN MAJALISAR DATTIJAWA TA AREWACIN ZAMFARA

**SUNAN AIKI:** Samar da ruwan aikin noman rani a Kaura Namoda

**KUƊIN AIKI:** N150M

**MATSAYIN AIKI:** An Aiwatar

Al'ummar wannan mazaɓa sun yi farin ciki da wannan aiki. Wannan aikin ya ƙunshi gina rijiyoyi wanda injuna zazu riƙa jawo ruwa ta butoci domin aikin ban-ruwa na noman rani. An ƙaddamar da wannan aikin ranar 31 ga watan Mayun shekarar 2020 a kan idanun ayarin ma'aikatanmu.

Waɗanda suka ci gajiyar aikin sun fito daga ƙananan hukumomin shiyyar mazaɓar, sune: Kaura Namoda, Zurmi, Shinkafi da Birnin Magaji. An raba kayan aiki guda 200 a kashi na farko da kuma ƙarin wannan adadin a kashi na biyu da kashi na ƙarshe, koda yake ba anyi raba daidai ba ne. Tsarin rabon kayayyakin ya dogara ne da girman ko wace ƙaramar hukuma. A bisa wannan tsarin Karamar Hukumar Kaura Namoda ce ta samu rabo mafi tsoka. Abun damuwa dai shine yadda aka tsinto waɗanda suk ci gajiyar shirin. A haƙiƙanin gaskiya mafi yawan waɗanda suka ci gajiyar shirin sune magoya bayan siyasar ɗan majalisar.









# MAZAƁAR GUSAU/TSAFE

SUNAN AIKI: Shirin Tallafa Wa Al'umma A Gusau
KUƊIN AIKI: N64m
MATSAYIN AIKI: An Aiwatar

Masu bin diddiƙin ayyuka sun halarci ƙauyen Kotonon Shehi a ranar 11 ga watan Fabrairun shekarar 2020 inda ɗan majalisa Kabiru Amadu ya rarraba waɗannan kayayyakin tallafi ga jama'ar Karamar Hukumar Gusau: injunan niƙa guda hamsin (50) da kekunan ɗinki samfurin "Butterfly" guda hamsin (50) da injunan janareton wutar lantarki guda talatin (30) da kayan yin aski irin na zamani guda talatin (30) da babura guda hamsin (50), da kuma kayan masarufi da suka haɗa da katin-katin na taliya da mangyada.

Babban abun damuwa shine mafi yawan waɗanda suka ci gajiyar shirin an tsinto su ne ba bisa wani tsari mai hujja ba. Muna iya tabbatar da cewa mafi yawan waɗanda suka ci gajiar shirin sune 'yan koren siyasar ɗan majalisar.





# MAZAƁAR GUSAU/TSAFE

SUNANAIKI: **Shirin Tallafa ma Al'umma a Tsafe**
KUƊIN AIKI: N64m
MATSAYIN AIKI: An Aiwatar



A ranar 10 ga watan Afrilun shekara ta 2020 masu bin diddiƙin ayyukan raya-ƙasa na mazaɓu sun halarci wurin da ɗan majalisa Kabiru Amadu ya rarraba kayayyakin tallafi ga al'ummar mazaɓar daga Karamar Hukumar Tsafe. Kayayyakin sun haɗa da babura, da kekunan ɗinki, da injunan janareto da kayn abinci waɗanda suka haɗa da taliya da man-girki. Abun damuwa shine yadda aka zaɓo wanɗanda suka ci gajiyar shirin. Zamu iya cewa a haƙiƙanin gaskiya mafi yawancin su magoya bayan ɗan majalisar ne.



# MAZAƊBAR BAKURA/MARADUN



**SUNAN AIKI:** Horas da Matasa aikin shirya fina-finai a Bakura/ Maradun
**KUƊIN AIKI:** N45m
**MATSAYIN AIKI:** An Aiwatar

A ranar 1 ga watan Fabrairun shekarar 2020 masu bin diddiƙin yadda ake gudanar da ayyukan raya-ƙasa sun halarci wurin da aka ƙaddamar da wannan aiki. Matasa guda ɗari (100) ne, waɗanda suka fito daga ƙananan hukumomi biyun da suka ƙunshi mazaɓar ne suka ci gajiyar shirin. An koyar da mahalarta wannan horon yadda ake tsare-tsaren maudu'in finai-finai.

Wannan aikin asara ne karara ga wannan mazaɓa, wanda ke nuna rashin tsarin yin la'akari da bukatun al'umma kamin a gabatar da ayyukan mazaɓu. Ma'aikatanmu sun tuntuɓi mahalarta horon kuma sun fahimci cewa basu da wani ilimi ko ƙwarewa a harkar yin fina-finai da zai bukaci irin wannan horon. Tabbatan, tsarin wannan horon bai ma cancanci kuɗin da aka ware ma aikin ba.

Wannan mazaɓa na daga cikin yankunan da suke baya wajen samun abubuwan more rayuwa a cikin jihar. Mazaɓar ba tada hanyoyi da ruwan sha na fanfo da wutar lantarki. Zai fi dacewa ne ayi amfani da irin waɗannan ayyukan raya ƙasa wajen cika giɓin rashin abubuwan more rayuwa ba yin almubazzaranci da dukiya a kan irin waɗannan ayyukan bada horon yin fina-finai ba.

# MAZAƁAR BAKURA/MARADUN

**SUNAN AIKI:** **Shirin horas da Matasa da Mata harkar watsa labarai da tace fina-finai da kyautata tarbiyya da kuma bunƙasa tattalin arziki**

**KUƊIN AIKI:** N45m
**MATSAYIN AIKI:** An Aiwatar

An gudanar da wannan shiri ne a ranar 2 ga watan Fabrairun shekarar 2020 bayan da aka gudanar da kashin farko (a jiya) a ranar 1 ga wannan watan, dukan su a wuri guda. Mun kuma lura da cewa matasan da aka horar a ranar farko sune kuma aka sake ba horo a wannan karon inda aka mayar da hankali kan yadda ake shirya fina-finai da tace su.

Wannan shirin kamar kashin na farko ɓarnar dukiya ce kawai saboda rashin tsarin tantance bukatun al'umma. Ma'aikatan mu sun tattauna da wasu da suka halarci horon kuma sun fahimci cewa basu da wani ilimi ko ƙwarewa a kan shirin fina-finai da zai sa a basu irin wannan horon.



# MAZAƁAR BAKURA/MARADUN

**SUNAN AIKI:** **Koyar da amfani da intanet wajen magance kalaman nuna ƙiyayya a mazaɓar tarayya ta Bakura/Maradun**

**KUƊIN AIKI:** N35m

**MATSAYIN AIKI:** An Aiwatar



An gudanar da wannan shiri ne a ranar 3 ga watan Fabrairun shekara ta 2020, wanda shi ne kashin ƙarshe na ayyukan horo uku da aka tsara yi a mazaɓar. Waɗanda suka halarci horarwa biyu a baya, sune kuma suka ci gajiyar wannan horon, kuma duka ayyukan horarwar guda uku an gudanar da su a wuri ɗaya kuma ɗan kwangila guda ne ya tafiyar da dukkan tsate-tsaren su. Wannan aiki bai yi daidai da bukatun al'ummar mazaɓar ba. Kananan Hukumomin Bakura da Maradun suna kunshe da karkara wadda ke bukatar abubuwan more rayuwa ne. Wannan aiki ya kasance maras amfanu domin ya kauce ma bukatun al'ummar mazaɓar.

Ma'aikatanmu sun shawarci al'ummar wannan mazaɓar da su riƙa tuntubar wakilansu domin samun ayyukan da za suyi masu amfani. Duka ayyukan horaswa guda ukun ba su da wani amfani ga bukatun mazaɓar. Kuɗaɗen da aka ware ma waɗannan ayyukan sun fi ƙarfin shirye-shiryen da aka aiwatar.

# MAZAƁAR TARAYYA TA KAURA/BIRNIN MAGAJI

**SUNAN AIKI:** Tallafa ma waɗanda rigingimu suka rutsa da su a mazaɓar tarayya ta Kaura/Birnin Magaji

**KUƊIN AIKI:** N95m

**MATSAYIN AIKI:** An Aiwatar




A ranar 16 ga watan Maris wakilanmu sun je Hedikwatar Jam'iyyar PDP ta Karamar Hukumar Kaura inda aka shirya ƙaddamar da shirin. An rarraba babura da injunan niƙa da wasu kayayyakin agaji. Kayayyakin na agaji dai domin a ba waɗanda bala'in rigingimu ya rutsa da su ne a cikin mazaɓar amma sai muka gano cewa waɗanda suka ci gajiyar shirin suna daga cikin magoya bayan dan majalisar ne.

Da a ce an aiwatar da waɗannan shirin kamar yadda ya dace, da sun taimaka ma waɗanda suka tagayyara a dalilin rigingimu, inda ma fi yawansu sun fito daga Karamar Hukumar Birnin Magaji ne.







# MAZAƊAR GUMMI/BUKKUYUM

SUNAN AIKI: **Samar da kekunan Napep da babura a yankin Karamar Hukumar Gummi**

KUƊIN AIKI: N75m

MATSAYIN AIKI: **An Aiwatar**

Karamar Hukumar Gummi ita ce mafi nisa daga Gusau, Hedkwatar jiha. Mafi yawan yankin ta karkara ce inda babu kayayyakin more rayuwa daga ɓangaren gwamnatin tarayya da ta jiha. Wannan shirin na bada tallafi zai iya zama mai amfani in aka yi la'akari da ƙuncin rayuwa da ake fama dashi a cikin sassan ƙaramar hukumar.

Wakilanmu sun halarci taron rarraba waɗannan kayayyaki a ranar 14 ga watan Mayu na shekarar 2020 inda aka rarraba kekunan NAPEP guda 10 da Babura. Sai dai saboda rashin sahihin tsari wajen rabon, kusan duk waɗanda suka ci gajiyar samun ababen hawan 'yan siyasa ne magoya bayan ɗan majalisar ba talakawa bane waɗanda suka cancanta su ci gajiyar shirin.



# MAZAƁAR GUMMI/BUKKUYUM

SUNAN AIKI: Samar da kekunan Napep da babura a yankin Karamar Hukumar Bukkuyum

KUƊIN AIKI: N50m

MATSAYIN AIKI: An Aiwatar



Mafi yawan ƙaramar hukumar ta Bukkuyum karkara ce inda babu abubuwan more rayuwa daga gwamnatin jiha ko ta tarayya. Yankin na fama da zaizayar ƙasa kuma yana matuƙar bukatar hanyoyi da gadoji. ZamTracka na ganin cewa wannan shiri na yunƙurin bada tallafi zai iya kyautata rayuwar da bunƙasa tattalin arzikin jama'ar ƙaramar hukumar.

Wakilanmu sun halarci bukin ƙaddamar da rabon kekunan na NAPEP guda 9 da babura 53 wanda aka yi a ranar 15 ga watan Mayun shekarar 2020. Sai dai 'yan siyasa masu goyon bayan ɗan majalisan ne amma ba waɗanda suka cancanci a ba taimako ba ne suka ci gajiyar shirin.

# MAZAƁARANKA/ MAFARA

SUNAN AIKI: **Kammala aikin ginin ɗakin kallon talabijin a Mazaɓar Anka/Mafara**

KUƊIN AIKI: **N62m**

MATSAYIN AIKI: **Ba a san inda za a gudanar da aikin ba**

Wannan aiki, duk da rashin alfanunshi ga al'ummar mazaɓar, babu cikakken bayanin wurin da za'a aiwatar balle abi diddiƙin aikin. Mun tuntuɓi al'ummar mazaɓar amma ba wani da ke da masaniyar aikin balle maganar kammalawa duk da cewa ana nuni da aikin na gudana.

SUNANAIKI: **Bada Tallafin Yin Fina-Finai ga Matasa da Mata**

KU[INAIKI: **N63M**

MATSAYIN AIKI: **Ba ayi ba**

Ba'a aiwatar da wannan shiri ba. A haƙiƙanin gaskiya, a yayinda ma'aikatanmu suka tuntuɓi al'ummar mazaɓar, sun yi matuƙar al'ajabi domin babu wani tallafi da aka ba wani a bisa wannan shirin.

# MAZAƁARMARU/BUNGUDU

SUNANAIKI: **Samar da Kekunan Napep a Dansadau Cikin Mazaɓar Maru/Bungudu**

KUƊIN AIKI: **N44.22m**

MATSAYIN AIKI: **Ba a Tantance Aiwatar da Aikin ba**

An tsara ƙaddamar da wannan shiri ne a garin Dansadau. Dansadau dai na cikin yankunan da ayyukan ta'addanci suka yi ƙamari, a saboda dalilan rashin tsaro ma'aikatanmu basu iya bin sawun shirin ba. Amma duk da haka, mun gana da mutanen da ke zaune a wannan gari domin tantance ko an aiwatar da shirin amma duk bayanai da muka samu na nuni da cewa ba a aiwatar ba.

# MAZAƁAR MARU/BUNGUDU

**SUNAN AIKI:** Bayar da Tallafin Koyon Sana'a ga Matasa da MataaMazaɓar Tarayya ta Maru/ Bungudu
**KUƊIN AIKI:**N32m
**MATSAYIN AIKI:**An Aiwatar




A ranar 7 ga watan Nuwambar shekara 2020 ma'aikatanmu suka bi sawun shirin. Samari guda ɗari (100) ne waɗanda suka haɗa da mata su kaci gajiyar wannan tallafi. Kayan da aka rarraba sune kekunan ɗinki guda ashirin (20) da injunan niƙa guda talatin (30) da babura guda hamsin (50).




Wasu mutum hamsin kuma sun samu tallafin kuɗi Naira dubu ɗari (N100,000) domin su bunƙasa jarin sana'o'insu. Ma'aikatanmu sun tattauna da wasu da aka ba tallafin waɗanda suka nuna farin ciki, balantana waɗanda suka samu tallafin kuɗi. Sun bayyana cewa wannan shine babban tallafi da suka taɓa samu, su kuma ma'aikatanmu sun shawarcesu da suyi amfani da tallafin ta hanyoyin da suka dace. Amma kamar yadda yake faruwa a wurare daban-daban, mafi yawan waɗanda suka ci gajiyar sun kasance magoya bayan ɗan majalisar ne.

# MAZAƊAR SHINKAFI/ ZURMI

SUNAN AIKI: Haƙa Rijiyoyin Burtsatse a Mazaɓar Tarayya ta Shinkafi/Zurmi
KUƊIN AIKI: N13m
MATSAYIN AIKI: An Aiwatar





Wannan mazaɓa na cikin lungu wadda kuma ke fama da hare-hare na ta'addanci. A ranar 18 ga watan Mayun shekarar 2020 ma'aikatanmu sun bi sawun wannan aiki a cikin sassan mazaɓar. Mun lura cewa wannan aikin ya haɗa ne da haƙa wasu sababbin rijiyoyin burtsatse da kuma gyara wasu tsofaffin da ke da matsaloli. Mun shawarci al'ummar mazaɓar da su riƙa kai kokensu domin a san matsalolin da suka dame su.

Ayyuka guda biyar ne a cikin wannan shirin aka tanadar ma wannan mazaɓar, amma saboda ayyukan ta'addanci da su kayi ƙamari a yanki ya tilasta ma ma'aikatanmu soke shirye-shiyen su na bin sawun duka ayyukan guda biyar na mazaɓar.

# MAZAƁAR MARU/ BUNGUDU

**SUNAN AIKI:** Horas da Matasa da Mata Sana'o'i a Mazaɓar Tarayya ta Maru/Bungudu
**KUƊIN AIKI:** N50m
**MATSAYIN AIKI:** An Aiwatar

An ƙaddamar da wannan shirin koyar da sana'o'i a ranar 18 ga watan Yunin shekarar 2020. Matasa guda ɗari (100) ne daga mazaɓar a ka koyar ma sana'o'in ɗinkin keke, sarrafa kwamfuta, da yadda ake yin sabulun wanki. A ƙarshen shirin koyarwar, an miƙa ma mahalarta horon tallafin kayayyakin aikin irin sana'o'in da aka yi masu horo akai.








# Manyan Ƙalubalen da aka Fuskanta

## Rashin Tsaro

Jihar Zamfara na daga cikin wuraren da ayyukan ta'addanci suka yi kamari a cikin yankin arewa maso yamma wanda hakan ya haifar da bala'o'i da dama. Wannan matsala ta hana ma'aikatan mu tuntuɓar al'ummomi da bin diddiƙin ayyuka a mazaɓun da cikin wannan hali. A misali, ma'aikatan mu basu iya shiga sassan ƙananan hukomomin Shinkafi da Zurmi ba don bin diddiƙin ayyuka. Wannan babbar ƙalubale ne kuma muna fatar yanayin tsaro zai inganta.

## Bayar da Fifiko ga Ayyukan Tallafi

Ayyukan tallafi abubuwa ne na wucin-gadi da zasu iya biyan bukatu na ɗaiɗaikun mutane ba tare da share hawayen alumma ba sune suka fi yawa a nan. Ma'aikatanmu sun fuskanci ƙalubalen bin sawu da tantancesu saboda babu wani cikakken tsari da aka samar na zaɓen mutanen wanda a hasali ma mafi yawan waɗanda suka ci gajiyar ayyukan ma'abutan siyasa ne ba waɗanda ke da matuƙar bukatar agaji ba.

## Rashin Takamaimen Bayanin Wurin Gudanar da Ayyuka

Domin ingancin bin diddiƙin ayyuka, ya kamata a samu bayanai na wuraren da za'a aiwatar dasu a cikin kasafin kuɗi. Amma abin takaici, babu bayanai na wuraren yin ayyukan kuma a dalilin haka al'ummmomi da ƙungiyoyi kan fuskanci wahalhalu wajen ƙoƙarin bin diddiƙin ayyukan da ganin cewa an aiwatar da su kamar yadda ya kamata. Wani misali da zamu iya nunawa shine na aikin samar da wutar lantarki mai aiki da hasken rana da injunan tiransifoma guda biyu a cikin Karamar Hukumar Bakura wanda aka ware ma kuɗi Naira Miliyan Ɗari Biyu da Goma Sha-Hudu da Budu Ɗari Biyu da Tamanin (N214.28m)

**N557m**

Daga cikin Naira Biliyan 1.42 da aka ware domin gudanar da ayyukan mazaɓu a Zamfara aka kashe wajen ayyukan bada tallafi da horaswa

**N164.22m**

Shine kuɗin ayyukan da ba a bi diddiƙinsu ba saboda halin rashin tsaro.

# A Taƙaice....

## Wayar da Kan Jama'a:

Wani ƙalubalen da ke yin tarnaƙi wajen saamun nasarar waɗannan ayyukan raya-ƙasa shine rashin fahimtar da al'ummomi game da su da kuma rashin tsarin wayar da kai tare da shigar da al'ummomin wajen ƙirkoro wa da aiwatar da ayyukan. Don haka ne, mafi wayan ayyukan basu da fuskanci manyan matsalolin mazaɓun ba.

## Kasafin Kudi da Cikakken Bayanai:

Ya kamata ne a shigar da sunayen wuraren da za ayi ayyukan cikin kasafin kuɗi don samar da cikakkun bayanai ga jama'a da ƙungiyoyi. Kamar yadda muka lura cewa kasafin kuɗin na ɗauke da sunayen ayyukan da kuɗaɗensu amma babu takamaiman wuraren da za'a aiwatar da ayyukan. Irin wannan halin ne ke bada ƙofar yin almubazzaranci da dukiya da kuma cin-hanci da rashawa.

**N98m**

**Shine Adadin Kuɗaɗen Ayyukan da ba a yi ba**

ZamTracka

Data | Civic Advocacy | Social Accountability

Follow up and track implementation of public projects within your vicinity

Upload pictures, add comments, send feedback to institutions

Announce and share with your friends, family and thousand across the state

Continue to engage.

No. 40, Sadiqu Sadiq Road,
Tudun Wada, Gusau, Zamfara State.

@ZamTracka

ZamTracka@gmail.com

# #AskQuestions